ZARIA JOURNAL OF LIBERAL ARTS
ZAJOLA
ISSN (print: ): 2141-3584 ISSN (online): 3121-7877
Journal of the Faculty of Arts
Ahmadu Bello University • Zaria • Nigeria
https://journals.abu.edu.ng/index.php/zajola Vol. 14, No. 1, June, 2026

# Tasirin Daidaita Rubutu ga Al'umma: Tsokaci daga harshen Hausa

***Salisu GARBA* & *Hauwa Muhammad BUGAJE***
Sashen Harsuna da Al'adun Afirka
Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya
salisukargi@gmail.com | hhmbugaje@gamil.com

## Tsakure
*Sanannen abu ne cewa harshe shi ne mafi girman ni'imar da Ubangiji ya yi wa ɗan'adam baiwa da ita don kyautata rayuwarsu da kyautata fahimtar junansu. Wannan kuma shi ne sinadarin more rayuwar ɗan'adam da ci gabansa da bunƙasarsa ta kowace fuska ta rayuwa. Rubutu kuwa hanya ce ta isar da saƙo cikin alamu musamman zuwa ga wanda yake nesa. Watau wanda wurin rayuwarsu ko zamanin rayuwarsu ya bambanta. Sannan kuma ga shi ana buƙatar rubutu ya iya wakiltar murya wacce kuma take cancanzawa daga wani lafazi ko yanayi zuwa wani. Bugu da ƙari kuma shi rubutu ba a iya maimaita shi don inganta fahimtar wanda aka yi wa saboda tazarar da ke tsakaninsu. Don haka dole ne a samar da wani daidaitaccen salo na baiɗaya wanda zai iya wakiltar kowace murya a kowane yanayi kuma ya sauƙaƙe hanyar hulɗa a tsakanin al'umma. Shi kuwa daidaitaccen rubutu, shi ne salon rubutun da aka yi tanajin ƙa'idoji da dokokin da za a sarrafa harshe da su. Daidaita rubutu shi ne yake bayar da damar iya bincike da rubuce-rubuce a cikin harshen al'umma, sannan kuma a iya koyo da koyar da shi. Waɗannan abubuwa da aka ambata game da harshe su ne ginshiƙan haɓaka da bunƙasar kowane harshe na duniya da kuma ci gaban al'umma ta kowace fuska. Wannan dalili ne ya sanya wannan maƙala ƙoƙarin zaƙulo ire-iren waɗannan fa'idoji, musamman ga harshen Hausa da al'ummar Hausawa domin jawo hankalin al'ummar Hausawa game da ƙara kula da tsare wannan muhimmin aiki ga harshen Hausa. Sannan kuma maƙalar ta faɗakar da Hausawa dangane da sakaci ko watsi da irin wannan muhimmin aiki da kuma zaƙulo irin haɗarin da ke tattare da haka.*
**Muhimman kalmomi:** *Daidaita rubutu, Harshen Hausa.*

## Gabatarwa
Tamkar yadda aka sani cewa harshe shi ne mafi girman ni'imar da Ubangiji ya yi wa ɗan'adam baiwa da ita, musamman ta fuskar sadarwa, don kyautata rayuwarsa da kyautata fahimtar juna. Haka kuma samuwar al'umma ita ce mafi girman inuwar

da ɗan'adam yake iya rayuwa a cikinta kuma tushen ɓuɓɓugar da harshe. Har ila yau, al'umma ita ce mafi girman muhallin da harshe ke iya rayuwa, har ya yi tasiri. Wannan girman matsayi na al'umma a kan samuwa da tasirin harshe, shi ne ya ba al'umma damar walwala a kan harshe. Saboda wannan muhimmin matsayi na al'umma ne ya sa suke iya sarrafa harshe duk ta yadda suke buƙata domin isar da saƙonni da nishaɗantarwa da sauran buƙatu a tsakaninsu.

A ɗaya ɓangaren kuma, yadda al'umma take da tasiri a kan harshe, haka shi ma harshe idan ya cika, ya tumbatsa kuma ya bunƙasa yake iya juya al'umma, ya haifar da al'amura masu dama a gare ta, waɗanda za su taimaka wajen kyautata rayuwarta da bunƙasarta. Babban misali a nan, shi ne, yadda bunƙasar harshe da haɓakarsa ke tilasta wa al'ummarsa samar masa da hanyar rubutu har kuma ta kai ga daidaita wannan rubutun domin isar da gamsasshen saƙo da kyautata al'amuran sadarwa a tsakaninsu. Samuwar haka kuma shi ne sinadarin more rayuwar ɗan'adam da ci gabansa da bunƙasarsa ta kowace fuska.

Rubutu kuwa, hanya ce ta isar da saƙo cikin alamu, musamman zuwa ga wanda yake nesa, ko dai ta fuskar wurin rayuwarsa ko kuma ta zamanin rayuwa gaba ɗaya. Bugu da ƙari kuma, ana buƙatar rubutu ya iya wakiltar haƙaƙanin muryar zance ne. Alhali kuwa ita murya, tana cancanzawa daga lafazi zuwa lafazi, ko daga yanayi zuwa wani. Sannan kuma shi rubutu ba a iya maimaita shi, don inganta fahimtar wanda aka yi wa saboda tazarar da ke tsakaninsu. Don haka dole ne a samar da wani daidaitaccen salo na baiɗaya wanda zai iya wakiltar kowace murya a kowane yanayi kuma ya sauƙaƙe hanyar hulɗa a tsakanin al'umma.

Shi kuwa daidaitaccen rubutu, shi ne salon rubutun da aka yi masa tanajin zaunannun ƙa'idoji da dokokin da za a sarrafa harshe da su. Daidaita rubutu, shi ne yake bayar da damar iya bincike da rubuce-rubuce a cikin harshen al'umma, sannan kuma a iya koyo da koyar da shi. Waɗannan abubuwa da aka ambata game da harshe su ne ginshiƙan haɓaka da bunƙasar kowane harshe na duniya da kuma ci gaban al'umma ta kowace fuska.

Wannan dalili ne ya sanya wannan maƙala ƙoƙarin zaƙulo ire-iren waɗannan fa'idoji musamman ga harshen Hausa da al'ummar Hausawa domin jawo hankalin al'ummar game da ƙara kula da tsare wannan muhimmin aiki ga harshen Hausa. Sannan kuma maƙalar ta faɗakar da su dangane da sakaci ko watsi da irin wannan muhimmin aiki da tare da fayyace irin haɗari da barazanar da ke tattare da haka.

Samuwar wani salon rubutu a cikin harshe babbar alama ce da ke nuni zuwa ga bunƙasar wannan harshe da kuma al'ummarsa. Haka kuma, samar da rubutu a harshe hanya ce ta sauƙaƙe tafarkin isar da saƙo da adana shi. Tamkar yadda samuwar hanyar rubutu take da muhimmanci a cikin kowace al'umma, haka kuma daidaita rubutu zai ƙara sauƙaƙe hanyar isar da saƙo da kuma adana shi, ba tare da ƙari ko ragi ko kuma birkita manufar saƙo ba.

## Ma'ana da manufar daidaita rubutu

Daidaita rubutu shi ne tanajin ƙa'idoji da dokokin da za a alamta muryoyin magana da su yayin isar da saƙo. Watau tattalin haruffan da za a gina harshe da su da kuma sharuɗɗan harhaɗa su wajen gina kalmomi da jumloli. Misali daidaita ƙa'idojin nahawu shi ne tattalin siffofin harshe da rukunansu ta yadda za a iya bayyana ma'anoni da su. Ma'anonin nan, sababbi ne ko tsofaffi, na fasaha ne ko na kimiyya? Watau dole a tattali ƙa'idojin ginin kalmomi irin su; tsarin jam'i da jam'antawa ko jinsi da jinsantarwa. Ko kuma na "ƙa'idojin tasarifi ta yadda za a tanaji ƙa'idojin alaƙar sautuka da ginin kalma ko ginin jumla da ƙa'idar bambance rubutaccen abu da lafazinsa. Sai '

kuma a yi tanajin ƙa'idojin da za a dinga sarrafa gundarin kalmomi a kan su. Watau dokokin haɗe kalma da rabe ta da kuma muhallan kowace ƙa'ida. Ko kuma ƙa'idar ninkin kalmomi da kuma ma'anoninsu. (Zarruƙ:1993)

Alal haƙiƙa ya zama dole a samar da irin waɗannan ƙa'idoji a harshen Hausa kuma a yi tsaye wajen tsare su domin harshen Hausa harshe ne mai tafiya da raujin murya, har da layinta, don haka dole a tanaji yaya za a iya gane ire-irensu a rubuce domin a iya karanta su daidai, ba tare da ɓata kari ko layin muryar ba, wanda kuma haka na iya rusa manufar zance a rubuce. Idan har ba a sanya ƙa'ida an daidaita rubutu a ƙarƙashinta ba, to kowa zai rubuta abin da ya ga dama kuma a karanta masa yadda aka ga dama, wanda kuma yin haka zai wahalar da hanyar sadarwa a rubuce kuma fahimta za ta yi wuya, sannan kuma ya haifar da ruɗu a cikin al'umma, saboda mummunar fahimtar saƙo.

Bugu da ƙari kuma, ana daidaita rubutu ne saboda inganta fahimtar saƙo ga wanda yake nesa domin kauce wa neman ƙarin bayani ko maimai. Sannan kuma ana daidaita rubutu ne saboda rubutu ya iya wakiltar murya domin murya na sauyawa amma rubutu ba ya sauyawa. Bayan haka kuma, tunda dai rubutu saƙo ne, a cikin alamu, zuwa ga wanda ke nesa, dole a samar da wata hanya guda wadda za ta iya zayyana abin da ke cikin zuciyar mai saƙon daidai wa daida, ba tare da gurɓata ma'ana ko lafazi ba.

Wani dalili da zai tilasta daidaita rubutu shi ne, daidaita rubutu zai samar da muryoyi ko sautuka da za su iya wakiltar sautukan da babu irinsu a cikin harsunan da ke hulɗa da harshen Hausa, irin su harshen Larabci da Ingilishi da Faransanci. Misali babu waɗannan sautuka; *tsa* da *ɓa* da *'ya* da *kwa* da *ƙwa* da *gya* da *kya* da *ƙya* da *gwa*, a harsunan Larabci da Ingilishi. Tamkar yadda kuma babu sautukan *th* da *v* da *x* da *f* da *q* na harshen Ingilishi a cikin Hausa. To idan ba a zauna an daidaita hanyar rubuta su a cikin Hausa ba, to duk kalmomin da suka shigo Hausa daga Ingilishi masu irin waɗannan kalmomi, to, ko dai Bahaushe ya haƙura da su ko kuma ya san wata dabara ta daban. Alhali kuwa yin watsi da su haifar da wata irin ƙatuwar naƙasu ce da kuma wagegen giɓi game da bunƙasar harshen Hausa, domin kuwa masana kimiyyar harshe sun tabbatar da cewa duk harshen da ba ya aro ko ba ya iya sarrafa kalmomin aro, to ya shirya daƙile kan sa ko macewa baki ɗaya.

Har wa yau, daidaita rubutu zai taimaka wajen samar da karin harshe ƙwara ɗaya madaidaici wanda zai yi wa kowa sauƙin rubuta saƙo da fahimtarsa cikin sauƙi. Sannan kuma za a sami damar kauce wa gamin gambiza da kwamacalar karin harshe mabambanta a wajen rubuta saƙwanni a cikin wannan harshe nasu. Misali, yayin da Kanawa da Zagezagi suke ƙoƙarin aika wa da rubutaccen saƙo da salon maganarsu, Kananci, haka kuma Katsinawa da Sakkwatawa za su aika da nasu, wanda kuma ana iya sarrafa kalmomi kama-rubutu ko kuma kalmomin farki ko na nahiya, waɗanda kuma sukan sami bambancin ma'ana. To irin wannan hali, wanne furuci ko ma'ana za a ɗauka, a matsayin haƙiƙanin manufar mai saƙo? Don haka, sai al'umma ta kasance cikin ruɗu da rashin fahimtar juna, wanda kuma zai iya haddasa ƙunci da durƙushewar al'umma.

## Muhimmancin Harshe

Masu iya magana kan ce, "Harshe tubalin ginin al'umma". Haƙiƙa harshe ginshiƙi ne na rayuwa, babban harsashi ne da rayuwa take bukata domin ta inganta. Kamar yadda sadarwa tsakanin mutum da mutum take wanzuwa ta amfani da harshe, haka ma sadarwa tsakanin mutum da mahaliccinsa take wakana ta amfani da harshe. Muhimmancin harshe ga ɗan'adam ba ya misaltuwa sai dai a kwatanta. Daga cikin muhimmancin da harshe yake da shi akwai sadarwa, wato isar da saƙo a magance ko a rubuce. Duk da cewa Ubangiji maɗaukakin sarki ya halicci harsuna ko mutane a ƙabilu daban-daban, amma wannan bai hana sadarwa tsananin mabambantan harsuna ba. Sai ma aka ƙara samun damar karkasa al'ummmomi da ƙara fahimtar juna ta la'ari da bambance-bambance da suke tsakanin harsuna.

Masana ilimin harshe ta fuskar zmantakewar al'umma sun bayyana muhimmancin harshe wajen samar da walwala a magana da kuma fito da dangantakar da take tskanin harshe da tunanin al'umma. Shahararren masanin harsuna mai suna Trudgill (1983) ya bayyana cewa cuɗanya tsakanin harsuna tana haifar da salo da irin lafazin da ake amfani da shi daga wani harshe zuwa wani. Shi kuwa Yakasai (2012) ya bayyana muhimmancin harshe ne ta la'akari da dangantakar da take wanzuwa tsakanin harshe da al'umma wadda ya kamanta da alaƙar da ke tsakanin rayuwa da ruhinta. Ya ƙara da bayyana cewa al'umma ba ta rayuwa sai da harshe, shi kuma harshe ba ya inganci a fagen sadarwa sai da ilimi.

Ilimin harshe shi yake bayar da dama a fitar da tsarin nahawun harshe, da fitar da ma'anonin kalmomi da dukkanin yadda ya kamata a tsara nazarin harshe a kimiyyance. Ilimin harshe yana bayar da dama wajen sanin ƙa'idojin rubuta harshe da na sadarwa a magance ko a rubuce da sanin hanyoyin raya harshe da ɗaukaka darajar harshe, har ma da kare harshe daga salwanta ko daga barazanar wasu harsunan da suke da tasiri a kansa. Tabbas kamar yadda ɗan'adam yake bukatar abinci domin ya rayu, haka yake bukatar harshe domin sadarwa.

**Taƙaitaccen Tarihin Samuwar Rubutu**

Rubutu suna ne na aikin zayyana ta hanyar amfani da alamomi ko surori ko kuma wasu haruffa da aka amince da su a harshe. Shi dai rubutu ƙirƙirarsa ake yi ta amfani da ilimi domin a fito da hanya karɓaɓɓiya da za a yi amfani da ita domin sadarwa a zayyane ba a magance ba. (Xavier 1995)

Rubutu yana ɗaya daga cikin hanyoyin sadarwa da Allah ya hore wa ɗan'adam sarrafa su domin isar da saƙo tsakanin mutum da mutum ko tsakanin al'umma da al'umma. Kafin samuwar rubutu, ɗan'adam yana sadarwa ne ta hanyar magana, sai dai ita magana tana biyan bukatar sadarwa ta nan take ne, kuma tsakanin mutanen da ke wuri ɗaya. Samuwar ilimin rubutu ya taimaka matuƙa wajen sauƙaƙa sadarwa tsakanin mutane da isar da saƙo cikin sauƙi tare da adana bayanai.

Samuwar rubutu ya zo wa ɗan'adam mataki-mataki ne tun daga fara rubutu ta hanyar zayyana alamomi da surori na abin da ake so a yi magana a kansa, har aka kai ga matakin amfani da haruffa wato baƙaƙe da wasula da kuma yadda amfani da waɗannan hanyoyi suka yi ta samun sauye-sauye daga lokaci zuwa lokaci. Kowace al'umma da nata tsarin rubutun, ko dai wanda suka ƙirƙiro ko kuma wanda suka ara daga wasu al'ummomi.

Bincike ya nuna cewa an fara rubutu kusan tun shekaru 50,000 da suka wuce, daga cikin waɗanda aka fara samun rubutunsu a wancan lokaci akwai mutanen Sin wato China, waɗanda suka ƙirƙiri rubutu a wancan lokaci ta amfani da alamomi na sawun tafiyar tsuntsaye ko surori da kuma alamomi daban-daban domin isar da saƙo. (Bunza, 2002)

Haka kuma, su ma Sumeriyawa sun daɗe da fara rubutu ta amfani da zana surar abin da suke so su yi magana a kansa. Misali sukan sarrafa surori 600 na halittu da alamomi daban-daban kamar a inda suke magana a kan doki sai su zana doki ko mutum ko ruwa da makamantan haka. Idan mutum ya ga zanen sai ya harhaɗa ya gane saƙon da ake so a isar.(Bunza,2002)

Tafiya ta yi tafiya rubutu ya samu har a ƙasar Misra dubban shekaru da suka shuɗe, sai dai su ma kamar Sinawa da Sumeriyawa, a wancan lokaci suna amfani da surori da alamomi ne wajen isar da saƙo. Idan za a iya tunawa a baya an bayyana cewa Sumeriyawa na amfani da surori 600 a rubutunsu, su kuma Misrawa suna amfani da surori 700 a wannan nau'in rubutu na zane a waɗancan zamunna da suka wuce. Idan aka yi maganar rubutu na haruffa wato rubutun abacada kuwa, bincike ya nuna cewa an fara wannan rubutu ne shekaru 3.400 da suka wuce, kuma Fonisawa ne suka ƙirƙire shi, wato mutanen ƙasar Phonesia can kusa da Syria. Su kuwa waɗannan mutane suna da baƙaƙe da wasulla 22 da suke amfani da su wajen rubuta harshensu a wancan lokaci, sannu a hankali Romawa suka fahimci wannan tsarin rubutu suka kuma kwaikwaye shi domin rubuta harshensu na Latin, sai dai su suna amfani da haruffa da wasula 23 ne wato sun yi ƙari a kan na Fonisawa. Tafiya ta yi tafiya, irin waɗannan haruffa suna samun karɓuwa har zamanin da Turawa su ma suka fahimci wannan tsarin rubutu, suka kwaikwaya domin rubuta harshensu na Turanci. Sai dai ko kafin Turawa su rubuta harshensu da tsarin rubutun 'abacada' Larabawa sun ƙirƙiro rubutun Larabci shekaru 2,000 da suka shuɗe wanda duk da cewa rubutu ne na amfani da haruffa da wasulla amma ya bambanta da rubutun 'abacada.'' (Bunza 2002).

**Samuwar Rubutu a Hausa**

Samuwar rubutu a Hausa yana da alaƙa da tarihin samuwar rubutu a duniya. Kamar yadda mawuyacin abu ne a iya kawo lokacin da aka fara rubutu a duniya, sai dai a yi hasashe, haka abin yake a Hausa, domin mawuyacin abu ne a iya tabbatar da sa'adda aka fara rubuta harshen Hausa da kuma salon rubutun da aka fara yi a Hausa. Wannan kuwa bai rasa nasaba da cewa babu wani gagarumin bincike da aka gudanar a wannan fanni na rubutun Hausa. Tabbatacciyar hujja da aka iya fi saurin

gabatarwa ita ce wadda take nuna an fara samun rubutu a Hausa bayan shigowar Musulunci ƙasar Hausa da aron haruffan Larabci aka ƙirƙiri rubutun ajami.

Kodayake an ɗan samu wasu hujjoji da suke nuna an taɓa rubuta harshen Hausa da harshen Girkanci da kuma yiwuwar rubuta shi da harshen Romanci wato Latin. Wannan bayani ya samu ne ta bakin shahararren ɗan siyasar nan kuma mai kishin Arewa wato malam Aminu Kano. An bayyana cewa malam Aminu Kano ya taɓa ganin wani tsohon rubutu da aka yi na Hausa da haruffan Girkanci a Ingila wanda ake hasashen an yi shi lokaci mai tsawo da ya wuce. Haka kuma, malam Aminu Kano ya tabbatar da wanzuwar wata rijiya a Kano da ke ɗauke da rubutun Romanci a jikinta wanda aka ce an yi tun zamanin daular Romawa. Wannan dalili ya sa malam Aminu Kano yake hasashen akwai yiyuwar rubuta Hausa tun a wancan lokaci ta amfani da tsarin rubutun waɗannan harsuna wato Girkanci da Romanci.

Fitaccen rubutu da ake amfani da shi a Hausa nau'i biyu ne wato rubutun ajami da na boko. Shi dai rubutun ajami rubutu ne da aka ari haruffan Larabci wajen rubuta furuci da maganar Hausa. Shi kuma rubutun boko rubutu ne da ake yi a Hausa ta amfani da haruffan abacada da Turawa suka ara daga Romawa suka rubuta harshensu, suka kuma ƙirƙiri rubutun Hausa a cikinsa.

Rubutun ajami kamar yadda aka bayyana ya samu ne tun bayan shigowar Musulunci da fahimtar ilimin addini a ƙasar Hausa a wuraren ƙarni na 15 ko na 16 har suwa na 17. Irin wannan rubutu ya sami karɓuwa da bunƙasa musamman a ƙarni na 18 zuwa na 19 har ma cikin ƙarni na 20.

Malaman addinin Musulunci da waɗannan ƙarnoni irin su malam Abdullahi Suka da malam Abubakar ibn Kutun-kura da sheik Ahmed Tila da sauransu suna daga sahun farko na malaman da suka yi wa Hausa gata wajen rubuta da babbaƙun Larabci tun a ƙarni na 17. Masu biye masu wajen wannan aiki sune shahararrun malaman addinin nan kuma marubuta waƙoƙin addini na ƙarni na 18 su malam Shi'itu ɗan Abdurra'uf da Muhammadu na Birnin Gwari da sauransu, su ma sun bunƙasa rubutun Hausa cikin ajami a ƙoƙarinsu na koyar da addinin Musulunci a ƙarnin da suka rayu. Har ila yau, tarihin rubuta Hausa cikin ajami ba zai kammala ba sai an yi la'akari da gagarumar gudummawar da malamai masu jihadi wato su sheik Usmanu Ɗanfodio da ƙaninsa Abdullahi Fodio da ɗansa Muhammadu Bello da autansa Isan Kware da 'yarsa Nana Asma'u da almajiransa irin su Muhammad Tukur da sauransu da ma masu biye masu irin su Attahirun Amadu suka bayar wajen yaɗa addinin Musulunci da samar da rubutu a cikin Hausa a fannoni daban

daban na ilimi. Haƙiƙa ba domin gudummawar waɗannan bayin Allah ba da rubutun Hausa ya ji kunya, (Yahya, 1988).

**Tarihin Daidaita Rubutun Hausa**

An daɗe ana rubuta Hausa da baƙaƙen boko ta hanyoyi daban-daban kafin a cim ma yarjejeniya wajen tabbatar da ƙa'idojin da ake bi a yanzu. Akwai abubuwa uku da suka sha wa masu ƙirƙirar rubutun Hausa na boko a wancan lokaci kai. Waɗannan abubuwa kuwa sun haɗa da matsalar furucin baƙaƙen da babu su a harshen ingilishi wato irin su 'ɗ' da 'ƙ' da ''y' da 'ts' da 'gw' da 'fy' da 'ky' da kuma 'kw' Haka kuma matsala ta biyu ita ce ta yadda ya kamata a haɗa kalma da kuma inda ya kamata a raba kalma. Har ila yau ga kuma matsalar karin harshe da yadda ake samun bambanci wajen wasu keɓaɓɓun kalmomi da suke da bambanci a kare-karen harshen Hausa, wanne ya dace a ɗauka a yi amfani da shi? Kuma ya za a yi ya sami karɓuwa ga sauran 'yan asalin harshen da ba su da wannan kalma? Da haka aka soma tattauna waɗannan matsaloli har aka cim ma samar da daidaito na ƙa'idar da ta dace.

Kafin a sami ƙa'idojin rubutu, yadda ake rubuta Hausa a wancan lokaci (kafin ƙarni na 20) ya sha bamban da yadda ake rubuta Hausa a yau, kuma kusan kowane marubuci da dabararsa. Misali an sami wani littafin J.F Schon (1885) mai suna *Magana Hausa*, inda ya rubuta wasu kalmomi da wasu ɗige-ɗige a ƙarƙashin wasu wasula, da kuma wasu alamomi masu nuna karin sauti na wasu kalmomin, har ma da haɗa kalmomin da a magance ko a rubuce bai kamata a haɗe su ba, misali a inda ya rubuta *tasi* a madadin *tashi*, da *sanu* a madadin *shanu*, da kuma *acikin* a madadin *a cikin.* Shi ma C.C H Robinson mai ƙamus na Nahawun Hausa da Frank Edgar mai littafin tatsuniyoyi na Hausa duk sun yi amfani da ɗige-ɗige ga haruffan da ba Ingilishi, kuma sun rubuta wasu kalmomin yadda suka fahimce su, ba yadda ɗan asalin harshe yake faɗi ba. (Yahaya 2002:124)

Kamar yadda aka gani, rubutun boko na Hausa na farko ya fara da matsala saboda ba 'yan asalin harshen suka fara rubuta shi ba. Wannan dalili ne ya sa daga bisani aka kawo masa ɗauki da nufin samun daidaito da fahimta ta bai ɗaya. Daga cikin waɗanda suka bayar da gudummawa akwai Hans Vischer (Dan Hausa) da Bargery G.P (1934) da Dr. R.M East da sauransu (ta ɓangaren Turawan mulkin mallaka). Haka kuma akwai ayyukan hukumar daidaita harshen Hausa wadda ta shirya tarurruka da dama domin kulawa da ƙa'dojin rubuta Hausa. Daga ciki akwai taron da aka yi a 1966 a Bamako ta ƙasar Mali da kuma wani taron da aka sake yi a jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya a 1970 da kuma wanda aka yi a Cibiyar Nazarin

Harsunan Nijeriya da ke Kano a 1972. Haka dai aka ci gaba da kawo wa rubutun Hausa ɗauki har rubutun ya kai ga matakin da yake a yau.

**Tasirin daidaita rubutu ga al'ummar Hausawa**

Bayan manufofin daidaita rubutu da suka gabata, waɗanda suke haskaka ɗimbin fa'idoji masu alaƙa da batun daidaita rubutu musamman ga harshen da aka daidaita rubutunsa da kuma al'ummar wannan harshe. A wannan muhalli za a ambaci wasu daga cikin gundarin tasirin da daidaita harshe ko rubutu yake yi ga al'umma domin ƙara fayyace gudunmuwarsa wajen bunƙasa harshe da al'ummarsa, kamar haka:

**Koyo da Koyarwa:** Daidata rubutu a harshe zai taimaka wajen sauƙaƙe koyo da koyarwa a cikin wannan harshe. Domin kuwa 'yan gida da baƙi kowa zai iya koyon harshen kuma ya naƙalce shi don haka zai sami sauƙin iya koyo da koyarwa a cikinsa. Samuwar haka kuwa shi ne babban sinadarin bunƙasar harshe da yaɗuwarsa, domin za a koye shi kuma a koyar, sannan kuma a yi rubuce-rubuce a cikinsa. Irin wannan damar ce ta taimaka wajen yaɗa al'adun al'ummar Hausawa da harshensu a cikin lungu da saƙon duniya, tamkar yadda yake wakana a Jami'o'i da sauran makarantun sassa daban-daban na duniya. Hakan kuma ya sanya al'adun Hausawa ƙayatar da al'ummomi masu ɗimbin yawa, har ya kai su ga kwaikwayon waɗannan al'adu na Hausawa.

**Bincike da Nazarce-Nazarce.** Daidaita rubutu a cikin harshe yana sauƙaƙa hanyoyin bincike na ilimi a cikinsa, musamman ga masana kimiyyar harshe waɗanda za su yi bincike game da siffofin harshen da dangoginsa da kuma fasalta shi, a cikin harsunan duniya da kuma yadda fasihai, masu ƙirƙiran ayyukan fasaha; waƙoƙi da labarai, wajen baje kolin hajarsu ta fasaha. Wannan ce ta taimaka wa harshen Hausa yin kafaɗa da kafaɗa da sauran manyan harsunan duniya kuma ta ba shi damar tsere wa tsara a fagagen ilimi da harkokin bincike. Haka kuma wannan dalili ya sauƙaƙe gudanar da bincike a cikin harshen Hausa, ba tare da buƙatar fassara ko tafintar wasu kalmomi ba. Irin wannan damar ce Turawan yawon shaƙatawa da na Mishan da kuma na Mulkin Mallaka suka yi amfani da ita suka naƙalci harshen Hausa tun kafin isowarsu ƙasar Hausa kuma suka yi hulɗa da Hausawa kai tsaye.

**Adanawa da Taskace Harshe.** Daidaita rubutu yana taimakawa wajen taskace dukkan abin da ya shafi harshe da al'ummarsa. Domin kuwa dukkan binciken da aka yi a cikinsa game da kimiyyarsa da adabinsa da al'adunsa, har da tarihin al'ummarsa, za a taskace su ne a rubuce kuma salon rubutun da kowa zai iya koya ya karanta. Masu iya magana kuwa na cewa: duk abin da aka rubuta shi ne tabbas,

wanda aka haddace kuwa, babu tabbas. Irin wannan damar ce ta taimaka aka sami bayanai masu yawa na harshen Hausa a taskace kuma a adane, wanda a yau zai yi wuya Hausawa su iya yi masa wannan gata.

**Zamanancewa:** harshe ba zai iya zamanancewa ba sai ya kasance yana da zaunannen tsari da dokoki kuma yana iya sarrafuwa a fagagen rayuwa daban-daban, sannan da kuma yawan al'umma. Duk waɗannan batutuwa ba za su tabbata, har a san da su ba, sai harshe yana da daidaitaccen rubutu. Sannan kuma sai harshe ya kasance zamanantacce ake amincewa a koyar da shi a makarantun ƙasa wanda kuma haka ne zai sanya a sanya shi a cikin kundin tsarin mulki a matsayin harshen ƙasa. Sanya shi a matsayin harshen ƙasa kuma shi ne zai sanya hukuma ta yi masa hidima, tun daga buga litattafai, da ɗaukan malaman da za su koyar da shi da ɗaukar nauyin ɗalibai masu karantawa da bincike a kan sa, har ya zuwa biyan kuɗin albashin masu koyar da shi.

Haka kuma zamanancewar harshe shi zai bayar da damar gudanar da aikin jarida da yaɗa labarai da shi. Gudanar da aikin jarida shi ne zai ba harshen damar yaɗuwa da mamaye sauran harsuna saboda yawaita saurarensa da karatunsa.

**Gogayya da Sauran Harsuna**

Daidaita rubutun harshe shi ne ke ba harshe damar gogayya, har da hamayya da sauran harsunan ƙasa 'yan uwansa, har ma sauran harsunan duniya a fagagen siyasar ƙasa da fagen ilimi da sauran fagagen rayuwa.

**Tasirin Daidaita harshe ga Al'umma.**

Bayan cin moriya iri daban-daban da harshe ke samu a sakamakon daidaita rubutunsa, haka kuma ita ma al'ummar da ke da harshen, ba a bar ta a baya ba wajen cin moriya mai tarin yawa sakamakon daidaita rubutun harshenta. Ga wasu daga cikin moriyar da Hausawa suka amfana da su a dalilin daidaita rubutun Hausa da aka yi:

**A Fagen Siyasa:**

**Daidaita harshen Hausa ya taimaka wa koyo da koyarwa da bincike**

Samuwar haka a harshen al'ummar Hausawa ya sanya aka san al'ummar Hausawa da al'adunta da tarihinta, sannan kuma ya ba ta damar yin tasiri a wajen gudanar da harkokin Nijeriya da ma sauran ƙasashen duniya. Wannan ce kuma ta bayar da dama har hukuma ta sanya harshen Hausa cikin *Harsunan Ƙasa* kuma take kashe masa kuɗaɗe a kan tsare-tsarensa. Samuwar haka ne ta sanya duniya ta iya ganin

dacewar harshen Hausa da zama *Harshen Hukuma* a Nijeriya kuma shi ne y aba harshen Hausa kasancewa *Harshen Hukuma* a ƙasar Jumhuriyar Nijer**.** Sannan kuma ta ba shi damar kasancewa *harshen hulɗa* a ƙasar Afirka bak ɗaya. Wannan dama tana haifar wa da al'ummar Hausawa tagomashi mai ɗimbin yawa a gida Nijeriya da Afirka da ma duniya baki ɗaya.

**A Fagen Tattalin Arziki:**

**a) Koyarwa:** idan aka daidaita rubutun harshe, shi ne zai bayar da dama a dinga koyar da harshen a makarantu kuma shi ne zai bayar da dama ga waɗanda suka karanta harshen Hausa samun aikin koyarwa. Samun aikin koyarwa a matsayin sana'a ga mutum zai bunƙasa tattalin arziƙinsa wannan kuma shi ne zai taimaka wajen bunƙasa tattalin arzikin al'ummar gabaɗayanta. Bugu da ƙari kuma zai bayar da dama ga Hausawa samun damar koyo da aikin koyarwa a sassa daban-daban na duniya. Misali yadda damar ta kai Hausawa irin su Farfesa Dandatti Abdulƙadir da Dalhatu Muhammad, da Muhammad Kabir Galadanci, da Maikuɗi Ƙaraye, da Salisu Yakasai, da Hafizu Miko Yakasai, da Aliyu Mu'azu, da Bello Alhassan, Da Muhammad Lawal Aminu, da Magaji Yakawada Tsoho, da Halliru Ahmad Amfani da sauransu da dama ƙasashen Turai da Amurka da Asia da ƙasashen Afirka da sassa daban-daban a gida Nijeriya. Tabbas! Wannan kuma zai taimaka wajen haɓakawa da bunƙasa tattalin arzikin ɗaiɗaikun Hausawa da kuma al'ummar Hausawa bakiɗayanta.

**b) Bincike:** Daidaita rubutu a cikin harshe shi ne zai buɗe hanyar gudanar da bincike a cikinsa. Gudanar da bincike a cikin harshe shi ne zai bayar da damar samun kuɗaɗen tallafi domin gudanar da bincike na musamman a cikinsa. Misali, yadda aka gudanar da bincike masu dama a harshen Hausa, irin su Dikshinare-Dikshinare da aka taskace kalmomin harshen, da kuma yadda aka taskace tatsuniyoyin Hausawa da al'adunsu masu tarin yawa. Samuwar wannan damar ta bunƙasa tattalin arzikin masu gudanar da binciken da masu taimaka musu domin dole sai aka wadata su da kuɗaɗen gudanar da rayuwarsu ta yau da kullum da kuma sayayyar wasu bayanai a hannun Hausawa, wanda hakan ya kai ga bunƙasa tattalin jama'ar da suke hulɗa da su, har ya kai ga al'ummar bakiɗayanta.

**c) Tallafin Karatu:** haka kuma sai an samar da hanyar rubutu ga harshe kuma an daidaita shi, sannan ɗalibai za su sami damar karanta harshen a matsayin darasi ko kwas mai zaman kan sa. Karanta shi kuma a matsayin darasi a manyan makarantu, shi ne zai ba waɗannan ɗalibai samun damar tallafi daga hukuma da kamfanoni da sauran ɗaiɗaikun masu ruwa da tsaki, na gida, da na waje, game da sha'anin wannan

harshe. Irin wannan tallafi ga ɗalibai zai taimaka musu iya zama da ƙafafunsu, wanda hakan kuma zai bunƙasa yalwatan arziƙi a cikin al'umma.

**d) Fina-Finai:** sai an samar da tsarin rubutu da daidaita shi sannan za a sami damar iya rubuta sikirif na wasan kwaikwato wanda za a iya juyar da shi a matsayin fim. Shiryawa da aiwatar da fim babbar hanya ce ta samar da kuɗaɗe masu tarin yawa ga hukuma da masu aiwatarwa da kuma kamfanonin da suke nuna shi da sauran masu harkokin kasuwanci a fagen fina-finai. A wani ƙiyasi da Farfesa Tsiga ya yi a shekara 2012, ya gano cewa shiryawa da aiwatar da fina-finan Hausa yana kawo wa Nijeriya kuɗin shiga har ƙimanin *Naira Biliyan goma (N10,000,000,000)* a matsayin kuɗin shiga. To su kuma 'ya'yan harshe da iyayensa nawa zai kawo musu? Saboda haka, samuwar irin wannan dama za ta taimaka matuƙa wajen haɓaka yalwatar dukiya a tsakanin al'ummar wannan harshe.

**e) Dandalin Sadarwa:** samar da rubutu a harshe da daidaita shi, shi ke bayar da dama a koyi harshen kuma a iya rubuta shi, sannan a iya amfani da shi a dandalin sadarwa. Amfani da harshen Hausa a dandalin sadarwa, musamman ta hanyar buɗe tashoshin *yutub da guruf,* ya bayar da damar bunƙasar harkokin kasuwancin data, ta hanyar aika wa da saƙwanni da samun magoya baya, wanda haka ke samar da kuɗaɗen shiga ta hanyar bunƙasar hada-hadar kasuwancin data, wanda kuma zai kai ga bunƙasa tattalin arzikin al'ummar wannan harshe.

**f) Aikin Jarida:** samuwar gidajen yaɗa labarai na rediyo da talbijin dole sai da daidaitaccen rubutu, musamman wajen rubuta labarai da tsarin sauran shirye-shirye, saboda hukuma ba za ta amince a yi amfani da wani salon rubutu wanda bai sami lamuncewarta ba. Wannan ce ta bayar da dama ga ma'aikatan yaɗa labarai Hausawa har da 'yan cin arziki, irin su Alhaji Halilu Ahmed Getso (na FRCN), da malam Aliyu Tanko da Halima Jumrau (na BBC) da Abdubaƙi Aliyu Jari (na TRT) suka shiga sassa daban-daban na duniya domin aikin yaɗa labarai, wanda kuma ya samar musu arziki da matsayi mai girma a wurin hukumomi da ma'aikatu daban-daban.

**g) Talifi da Ɗab'i:** daidaita rubutun harshe shi ne yake bayar da damar aiwatar da talifi a cikinsa. Samuwar talifi a cikinsa kuma shi zai samar da sana'a ga Mawallafa da Editoci da masu bugawa da masu talla da kuma aikin albashi a fagage daban-daban na ma'aikatun ɗab'i a cikin wannan al'umma. Irin wannan damar ce ta haifar da samuwar hukumomi da maɗaba'u daban-daban domin samarwa da buga litattafai da jaridu a ƙasar Hausa. Misalin haka ya haɗa da samuwar hukumar NORLA, wadda ta samar da litattafan *gasa* ta farko, *Ruwan Bagaja, Jiki Magayi,*

*Gandoki, Idon Matambayi* da sauran litattafai masu dama. Sai kuma Maɗaba'ar Gaskiya wadda ta samar da *Jaridar Gaskiya Ta fi Kwabo* da sauran litattafan karatu irin su *Magana Jari Ce, Tafiya Mabuɗin Ilimi, Bala da Babiya, Ƙaramin Sani* sauransu da dama.

**h) Horo da Horarwa:** samuwar daidaitaccen rubutu shi zai wajabta 'yan jarida da malaman makaranta da ma'aikatan shari'a da na gidajen talifi buƙatar horarwa daga ƙwararru a fagen harshen Hausa. Wannan kuma zai bayar da dama ga wasu rukuni na masana harshen Hausa samun ɗauli a hannun Gwamnati da hukumomi daban-daban kuma ya yi sanadiyyar yaɗuwar arziki a cikin al'ummar Hausawa.

**i) Haɗin Kan Al'umma:** duk da cewa ba kowane Bahaushe ne ya san da daidaitaccen rubutun Hausa ba, sai dai 'yan book kawai. Daidaitaccen rubutun na tilasta kowanensu ajiye Karin harshensa ya yi amfani da daidaitaccen rubutu. Haɗuwar irin wannan rukuni na Hausawa da hulɗa a tsakaninsu tana sauƙi kuma tana haɓaka fahintar juna a tsakaninsu.

**j) Sauƙaƙa Tafiyar da Al'umma:** samuwar daidaitaccen rubutu shi ne zai sauƙaƙa wa baƙi iya laƙantar harshe da kuma iya hulɗa da wannan al'umma a rubuce. Samuwar haka ce ta bayar da dama ga Turawan Mulkin Mallaka samun sauƙin gudanar da mulkinsu a ƙasar Hausa, ta yadda suka sami sauƙin koyon harshen a rubuce da kuma yadda suka dinga bayar da umurni a rubuce. Wannan ya taimaka musu matuƙa saboda maimakon koyon kowane Karin harshen a Hausa, sai su koyo daidaitacciyar Hausa da rubutunta kawai, su gudanar da mulkinsu da ita.

**Fagen Ilimi:**

Sanannen abu ne cewa, fassara ginshiƙi ce wajen samuwa da bunƙasar ilimin al'ummomi daban-daban a faɗin duniya. Haka nan samuwar daidaitaccen rubutu ya haɓaka aikin fassara a cikin harshen Hausa, musamman daga Larabci da Ingilishi zuwa Hausa, wanda kuma ya taimaka matuƙa wajen samuwa da bunƙasar ilimi a cikin al'ummar Hausawa.

**Kammalawa:**

Wannan muƙala ta ƙoƙarta fayyace ma'ana da manufa da tarihin samuwa da daidaita rubutu da bunƙasarsa. Haka kuma muƙalar ta ambaci yadda daidaita rubutu yake taimakawa wajen haɓaka da bunƙasar harshe. Sanna kuma ta ambaci yadda daidaita rubutu yake bayar da gagarumar gudunmuwa wajen bunƙasa al'umma ta fuskar tattalin arzikinta da sha'anin siyasarta da na iliminta. A ƙarshe muƙalar tana jawo hankalin al'ummar Hausawa lallai su duƙufa wajen ganin sun ci gaba da

bibiyan kyautata hanyar rubuta harshensu da bitarsa daga lokaci zuwa lokaci domin dacewa da dukkan yanayi da juyin zamani domin kada a bar su a baya. Musamman idan aka yi la'akari da irin farin jini da karɓuwa da sauƙin sarrafawa da Allah ya yi wa wannan harshe nasu gami da ƙwarewa da sauƙin kai na Hausawa wajen iya hulɗa da baƙi, ya sanya al'ummomin duniya suke rungumar harshen Hausa a matsayin harshen hulɗa.

**Manazarta**

Amin, M.L (2016), "Waiwaye Adon Tafiya: Sake Bitar Ƙa'idojin Rubutun Hausa." *Harshe 9, Journal of African Languages*, Zaria: Sashen Harsuna da Al'adun Afirka: Zaria, Jami'ar Ahmadu Bello.

Bugaje, H.M (2024) "Ƙa'idojin Rubutun Hausa, Ga Ƙoshi Ga Kwanan Yunwa" JOLLS. *International Journal of Arts, Language Linguistics and Literary Studies. Vol 12 (1)* Department of French, Faculty of Humanities: Owerri, Imo State University

Bunza, A. M. (2002). *Rubutun Hausa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrarash Islamic Publications Centre LTD.

Galadanci, M.K.M. (1976), *An Introduction to Hausa Grammar*. Zaria: Longman.

Kraft C. H. and Kirk-Greene A.H.M. (1990) *Teach Yourself Hausa. A Complete Course for Beginners*. London: Hodder and Stoughton Ltd.

Sani M. A. Z. (1999). *Tsarin Sauti da Nahawun Hausa*. Ibadan: University Press Plc.

Skinner, N. (2007). *A Grammar of Hausa for Nigerian Secondary Schools and Colleges*. Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Trudgill, P. (1983) Socio-Linguistics. 2nd Edition. Harmonds Worth Pengium Books

Wikipedia: https://en.wikipedia.org/wiki/Orthography

Wurma, A. G. (2005) *Daidaitacciyar Hausa da Ƙa'idojin Rubutunta*. Kaduna: Olatunde Rasheed Publishing Works

Yahaya, I. Y. (1988) *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zariya: Northern Nigerian Publishing Company Ltd.

Yakasai, S.A (2012), Jagoran Ilimin Walwalar Harshe. Sokoto: Garkuwa Media Services Ltd

Zaria, A. B. (2014) *Sabon Nahawun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Plc.

Zarruƙ, R. M. (1978) Tarihin Ƙa'idojin Rubutun Hausa (Ed) Yahaya, I. Y. and Rufa'i, A *Language and Literature in Hausa* Kano: Uniprinters Limited.

Zarruƙ, R. M. (1993), Aro da Ƙirƙira a Harshen Hausa. Institute of Education. Zaria Jami'ar Ahmadu Bello.